# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na takwas: Ana zaman ƙarya a birni

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | 'yar shekara 20 |
| Sa'adatu: | 'yar shekara 35 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Suleman: | ɗan shekara 19 |
| Kwastoma: | ɗan shekara 40 |
| Larai: | 'yar shekara 30 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, filin "Ji Ka Karu" na maraba da ku. Barkanmu da sake saduwa a kashi na takwas cikin wasan kwaikwayon da muke kawo muku ta wannan gidan rediyo mai taken "Tudun mun tsira - Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". A cikin wancan kashin da ya gabata ƙawar Lami Sa'adatu, wadda ake wa kallon mutuniyar kirki, ta ja Lami zuwa sayyaya wadda ga dukkan alamu tana da wani shiri a ƙasa. A can gida Afirka kuma, an sallami iyayen Lami daga aiki. To ko me zai faru? Tuni al'amarin ya fara tsamari. Bari mu ji abin da zai biyo baya a cikin wasan na yau mai suna "Ana zaman ƙarya a birni". Za mu fara wasan ne daga inda muka tsaya. Ga dai Lami can da Sa'adatu a kantin sayar da abinci suna tattaunawa.

**Fitowa ta 1: Lami da Sa'adatu a gidan cin abinci**

**Sa'adatu:** Idan kina son ki ji daɗin zama a Turai a matsayin baƙuwa wadda ba 'yar kasa ba, to fa sai kin 'yantar da kanki. Mutane kan yi hakan ta hanyoyi dabam-dabam.

**Lami:** Na 'yantar da kaina? Ban gane ba. Ai ni ta halartacciyar hanya na shigo ƙasar nan, da bizar karatu. In ba don haka ai ba zai yiwu na yi karatu a nan ba.

**Sa'adatu:** Shhhh! Ki zi magana ƙasa-ƙasa Lami. Na san kin zo nan a matsayin ɗaliba. Amma ai akwai ka'idoji da yawa a kan ɗalibai 'yan ƙasashen waje a kan abubuwan da aka yarda za su iya yi da abubuwan da ba za su iya yi ba. Abin da nake nufi shi ne, dole ki nemi matsayin 'yanci iri na kowane ɗan ƙasa. Abin da kike buƙata yanzu shi ne takardar izinin yin aiki. In kuwa ba ki da wannan, to rayuwarki fa sai yadda ta yiwu.

**Lami:** Ok. To wacce shawara za ki ba ni a kan hanyar da zan bi

na samu takardar?

**Sa'adatu:** Hanyar da za ki bi? A sa ki a lallai.

**Lami:** A sa ni a lallai?

**Sa'adatu:** Kwarai!

**Lami:** Kina nufin na yi aure?

**Sa'adatu:** E!

**Lami:** To amma wanne amfani aurena da Magaji zai yi mini wajen samun wannan damar a nan? Ban gane ba.

**Sa'adatu:** Hahaha! Kai lallai kanki na tukunya fiye da yadda na zata. Kin ga Lami, daga yanzu Magaji ba ya cikin lissafinki. Ke ma da kanki kin faɗa fa cewa ba shi da wani amfani a rayuwarki ta nan. Kina ji? Dole ki auri Bature.

**Lami:** Me? Sam! Haba Sa'adatu, me zai sa ki yi min wannan tunanin? Ba shakka muna nesa ni da Magaji, kuma na yi masa ƙarya a kan yadda rayuwa take da wahala a nan, amma duk da haka, har yanzu ina sonsa!

**Sa'adatu:** Kin ga, kwantar da hankalinki. Ba komai, ki ci gaba da sonsa. Ba matsala. Zan iya taimaka miki ki auri wani a asirce. Ba ma sai kun san juna kafin a yi bikin ba, ke ba ma sai kun haɗu ma ba kwata-kwata. Abin da za ku yi shi ne, za ku dinga yin kamar miji da mata kuke da shi. Da zarar an yi hakan, to ba da daɗewa ba za ki sami bizar izinin yin aiki, kin ga sai ki yi abin da kike so.

**Lami:** Haka ziƙau? Kai, anya kuwa haka ne? To me zan bayar ni kuma? Da farko kin ce sai na daure na kuma yi haƙuri a kan wasu abubuwa. To har yaushe zan daure, kuma a kan me zan yi haƙurin?

**Sa'adatu:** Mmm… Ok, kina da gaskiya. Akwai ɗan abin da za ki bayar, amma ba wani abu ba ne da zai gagare ki. Akwai ɗan abin da za ki biya mjin bizar.

**Lami:** Na biya shi? Na ɗauka maza su ya kamata su biya sadaki ga mata? Kuma ta yaya zan samu kuɗin da zan ba shi, ba wani aiki nake ba?

**Sa'adatu:** Kar ki damu! In dai kin amince da wannan tsarin, komai zai tafi daidai. Za ki dinga biyan kuɗin a hankali tun daga ranar da aka ɗaura auren har lokacin da za ki sami takardar izinin. Kin ji? A ɗan wannan tsakanin, dole ne ki yi haƙuri. Zan kuma samo miki aiki. Ba wata wahala.

**Lami:** Wato dai kamar na sayi takardar izinin ke nan ta hanyar auren biza. Haka ne?

**Sa'adatu:** Haka ne.

**Lami:** To amma Sa'a, idan shi wannan mijin bizar ya nemi wani abu da ni bayan kuɗin fa? Yaya zan yi? Ina nufin a ƙa'ida, tun da aure za a daura mana.

**Sa'adatu:** Ba zai nemi komai ba don kuwa ba shi da ikon yin hakan. In kuwa ya nemi hakan, to ya rage naki. Wasu mutanen daga auren biza sai kuma soyayya ta shiga. Komai na iya faruwa.

**Lami:** Sam! Ba dai ni ba. Ni karatu ne ya kawo ni nan. In kuwa na yanke shawarar bin wannan tsarin, zan yi hakan ne don samun kuɗin shigar da zan yi karatuna, na kuma ji daɗin rayuwata a nan.

**Sa'adatu:** Da kyau! Me kika ce? Za ki yi amfani da wannan damar?

**Lami:** Ban ce ba tukuna, Sa'a. Wannan yana buƙatar dogon tunani! Magana ce ta na yi aure. Ba abu ne na wasa ba. Ina buƙatar lokaci don na yi tunani.

**Sa'adatu:** Ya yi. Amma kada ki manta akwai 'yan'uwanmu da yawa a can gida Afirka waɗanda a shirye suke su sami irin wannan damar. ... O, don Allah, bari na amsa wayar nan, daga gida ne aka bugo. ... *Hello,* Sa'adatu ce ke magana.

**Malam Talle:** *Hello,* don Allah ki yi haƙuri, ni ne baban Lami. Ta kira ni da wannan lambar lokacin da ta zo Turai, kuma ganin cewa ke ƙawarta ce, sai nake tunanin ko zaki isar mini da saƙo gare ta?

**Sa'adatu:** An kuwa yi dace! Ina tare da ita a halin yanzu. Bari na haɗa ka da ita. ... Lami, babanki ne. Yana so ya yi magana da ke.

**Lami:** Baba! In ce ko dai lafiya?

**Malam Talle** Lafiya ƙalau Lami.

**Lami:** Allah na gode ma. Na ɗauka wani mummunan abu ne ya faru. To, wace magana za ka faɗa min?

**Malam Talle** Ba wai ina so na tayar miki da hankali ba ne, Lami, an sallame mu daga aiki da ni da babarki. Amma fa kada ki

| | |
|---|---|
| | damu, za mu san yadda ya mu yi. Ni dai na faɗa miki ne kawai don ya kamata ke ma ki sani. |
| **Lami:** | Allah Sarki, Baba, sai haƙuri! To yaya kuke yi ke nan? Amma abin ba daɗi. |
| **Malam Talle** | Muna… muna lallaɓawa, kada ki damu! Kin ga Lami, ba za mu iya yin wata doguwar magana ba don kuɗina sun kusa ƙarewa. Sai dai yan… |
| **Lami:** | Baba! Baba!! *Hello,* Baba , kana jina? …Kash! Ta yanke. |
| **Sa'adatu:** | Lami, me ya faru? |
| **Lami:** | Sama min aiki, Sa'adatu, maza-maza. Sannan kuma ki nemo min Baturen da zan aura ma. |

**Mai ba da labari:**
A can kuma Afirka ta Arewa tarzomar siyasa sai ƙaruwa take yi, kuma rikici ya ɓarke wanda hakan ya sa dubban mutane barin gidajensu suna neman mafaka a sansanonin 'yan gudun hijira. Faisal da Suleman ma na daga cikin waɗanda hargitsin ya rutsa da su, kuma hakan ya fara shafar abotarsu.

**Fitowa ta 2: Faisal da Suleman na tattaki a gaɓar teku**

| | |
|---|---|
| **Suleman:** | Faisal, ko teku ba a hayyacinta take kamar da ba. Ina jiye wa iyayena, da sauran dangina tsoro, da ƙasata, da ma mu kanmu. Ya kamata mu gudu fa tun muna da damar yin hakan. |
| **Faisal:** | To mu tafi ina? |

**Suleman:** Ina fa ka ce?! Ko'ina ma, in dai mun bar nan. Mutane da dama sun fantsama zuwa ƙasashe maƙwabta.

**Faisal:** Kasashe maƙwabta? Haba Suleman, muna ganin tashin hankali ta ko'ina a kullum. Abin da yake faruwa ɗin nan ba daɗi, amma yanayin zai ƙara taɓarɓarewa. Ɓa mu da tabbas ɗin cewa faɗan nan ba zai barbazu ko'ina ba. Wannan shi ne lokacin da ya fi dacewa mu yi ƙaura zuwa Turai.

**Suleman:** Haba Faisal! Kai har yanzu ba ka daina wannan mafarkin naka ba? Kasarmu na dab da afkawa cikin yaƙin basasa, amma ba ka da wani tunanin da ya wuce Turai? Duk da cewa rayuwa a Afirka ba daɗi, amma ita ce gida a wurinka. Ai ko ba komai ya kamata ka nuna kishinka.

**Faisal:** Kai! Ka ga, don Allah ka daina yi min wa'azi a kan abin da ya kamata na yi! Idan kana son tafiya wata ƙasa a Afirka, to bisimilla! Ni dai ba ni da sha'awar yin haka, Suleman. Ka fahimta ko? Ka yi harkarka kawai, na yi tawa!

**Suleman:** Ka ga kuwa zan fita daga harkarka. Kamata ma ya yi a ce na yi hakan tun tuni, amma yanzu ma ba ta ɓaci ba. Faisal, Allah Ya ba ka sa'a a wannan mafarkin naka na zuwa Turai!

**Faisal:** Suleman! Ji mana Suleman, don Allah ka yi haƙuri! Ka tsaya ni mana! Kada ka manta fa mu 'yan'uwan juna ne.

**Suleman:** Ai 'yan'uwa ba sa rabuwa. Kai kuwa kanka kawai ka sani!

**Faisal:** Suleman! Suleman!

**Mai ba da labari:**

A can kuma, Sa'adatu ba ta ɓata wani lokaci wajen nemo wa Lami aiki ba wadda take cikin tsananin buƙatar samun kuɗin shiga ba don taimaka wa kanta a Turai kawai ba, har ma da iyayenta da aka sallama daga aiki a gida Afirka. Bari mu bi Lami har wajen aikinta a karon farko inda ta sami wata ma'aikaciya 'yar gudun hijira daga Afirka mai suna Larai. Larai ta yi mata maraba.

**Fitowa ta 3: Lami da Sa'adatu a gidan rawa**

**Sa'adatu:** Yauwa! Abubuwa na tafiya kamar yadda ya kamata, Lami. Nan ne sabon wajen aikinki. Za ki dinga karɓar oda daga wurin kwastomomi kina kawo musu abin da suke buƙata. Shi ke nan. Idan kina da wata tambaya ne kuma, ga Larai nan. Yau shekararta uku ke nan tana aiki a nan. Allah Ya ba da sa'a!

**Lami:** Amma… wannan wajen …

**Larai:** Maraba, sannu da zuwa! Ni ce Larai.

**Lami:** Sannu da aiki, Larai, ni sunana Lami. Kina jin za mu kai kamar

**Larai:** Kada ki damu, za ki saba a hankali. Da farko za ki ji aikin kamar ki gudu, amma da kin saba, za ki yi mamakin irin kuɗin da za ki samu daga wajen kwastomimi a dare ɗaya kawai!

**Lami:** Kina jin za mu kai kamar ƙarfe nawa kafin mu tashi?

**Larai:** Aiki za mu yi ta yi har sai kowa ya fashe daga nan. Karshen sati ne, don haka wurin zai cika sosai yau. Ina jin ma za mu kai har safiya.

**Lami:** To nawa kuma kike ɗauka?

**Larai:** Ya danganta. Kin ga Lami, bai kamata ma in faɗa miki ba, amma ni ina aiki ne ba bisa ka'ida ba. Ba ni da takardar izinin aiki, don haka na dogara ne a kan abin da nake samu daga wajen kwastomomi. Ladan aikina ba wani abin a zo a gani ba ne. Wani lokacin ma ba a biyana. Mu je kawai mu yi aiki, ga wani kwastoma can yana ɗago hannu. Je ki ki same shi, ki ji me yake so.

**Mai gabatarwa:**

Wannan shi ne ƙarshen kashi na takwas daga cikin wasan kwaikwayonmu mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka masu ƙaura zuwa Turai". Shin gaskiya ne rayuwar Lami za ta inganta tun da yanzu ta sami aiki? Mene ne haƙiƙanin abin da Sa'adatu take samu daga cikin shirin da ta yi wa Lami? Kuma shin wannan shi ne ƙarshen abotar Faisal da Suleman?

Ku biyo mu zuwa kashi na gaba. Kafin nan, ku biyo mu a shafinmu na Facebook, wato facebook.com/dw.lbe.